# Book: Philemon

## Philemon

### Chapter 1

1 Bulus, daurarren Yesu Almasihu, da kuma dan'uwa Timotawus zuwa ga Filimon, kaunataccen abokinmu
da kuma abokin aikin mu, 2 da Afiya yar'uwanmu da Arkifus abokin aikin mu a filin daga, da kuma
Ikilisiyar da take taruwa a gidan ka: 3 Alheri da salama su kasance gare ka daga wurin Allah Ubanmu, da
Ubangiji Yesu Almasihu. 4 Kowane lokaci ina gode wa Allah. Ina ambaton ku cikin addu'oi na. 5 Na ji
labarin kauna da bangaskiya da ka ke da ita a cikin Ubangiji Yesu da dukkan yan'uwa masu bi. 6 Ina
addu'a zumuntar bangaskiyarka ta inganta ga kawo sanin kowane kyakkyawan abu dake cikin mu a cikin
Almasihu. 7 Na yi farinciki kwarai, na kuma ta'azantu saboda kaunarka, saboda zukatan masu bi sun
kwanta ta wurin ka, dan'uwa. 8 Saboda haka, ko da ya ke ina da gabagadi a cikin Almasihu domin in ba ka
umarni ka yi abinda ya kamata ka yi, 9 duk da haka sabo da kauna, na fi so in roke ka- Ni, Bulus, dattijo, a
yanzu kuma ga ni dan kurkuku domin Almasihu Yesu. 10 Ina rokon ka saboda da na Onisimus, wanda na
zama uba a gare shi sa'adda nake cikin sarkokina. 11 Domin a da kam, ba shi da amfani a wurin ka, amma
yanzu yana da amfani a gare ka da kuma a gare ni. 12 Na kuma aike shi wurinka, shi wanda ya ke a cikin
zuciyata kwarai. 13 Na so da na rike shi a wuri na, domin ya rika yi mini hidima a madadin ka, a lokacin
da ni ke cikin sarkoki saboda bishara. 14 Amma ba na so in yi wani abu ba tare da sanin ka ba. Ba ni so
nagarin aikinka ya zama na dole amma daga kyakkyawar nufi. 15 Watakila dalilin da yasa ya rabu da kai
na dan lokaci ke nan, domin ka karbe shi kuma har abada. 16 Daga yanzu ba za ya zama bawa ba kuma,
amma fiye da bawa, wato kaunataccen dan'uwa. Shi kaunatacce ne musamman a gare ni, har fiye da haka
ma a gare ka, a cikin jiki da kuma cikin Ubangiji. 17 Idan ka maishe ni abokin hidima, ka karbe shi kamar
yadda za ka karbe ni. 18 Idan kuwa ya yi maka abinda ba daidai ba ko kuwa kana bin sa wani abu, ka
dauka yana wurina. 19 Ni, Bulus, na rubuta wannan da hannuna: zan biya ka. Ba kuwa cewa sai na gaya
maka cewa ina bin ka bashin kanka ba. 20 I, dan'uwa, ka yi mani alheri cikin Ubangiji; ka ba zuciyata hutu
a cikin Almasihu. 21 Saboda Ina da tabbaci game da biyayyarka, na rubuta maka. Na san za ka yi fiye da
abinda na roka. 22 Harwayau, ka shirya mani masauki. Domin ina fata ta wurin adu'oinku, nan ba da
dadewa ba za a maida ni wurin ku. 23 Efafaras, abokina cikin Almasihu Yesu a kurkuku yana gaishe ka, 24
haka ma Markus da Aristarkus, da Dimas, da Luka abokan aikina. 25 Bari Alherin Ubangiji Yesu Almasihu
ya kasance da Ruhunka. Amin.

---


generated on Sun Mar 17 14:07:36 2024